# Littafi mai Tsarki na yara

**Ke gabatar da**



# Dawuda Sarkin (Sashi 1)


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**



**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.




**Dan saurayi Dawuda yana cikin gudu. Sarki Shawulu ya so ya kashe shi. Dawuda ya zauan a hamada, a wani katon kogo tare da masu binsa guda dari hudu. Wani lokaci, sojojin Sarki Shawulu sun kusa su same su. Amma Dawuda ya ci gaba da tafiya.**



Dan hidimar Shawulu mai suna Dowek, ya gaya wa sarki cewa firistoci su ne suka taimake Dawuda ya kubce. Shawulu ya ba da umarni a kakkashe su. Amma Dowek ne kadai yana da zuciya ya yi shi. Cikin wulakanci ya kakkashe firistoci tamanin da biyar da iyalinsu da takobinsa. Mugunta ne tsansa.



3

Wata rana, Shawulu yana farautar Dawuda sai ya kai har cikin kogon inda Dawuda da mazansa suke buya. Shawulu shi kadai ne!



4

A cikin kogon, da a ce Dawuda yana so, da ya kashe Shawulu cikin sauki. Maimaikon haka, sai ya je a hankali ya yanke gefen rigarsa da wukansa mai kaifi.



Sa'ad da Shawulu ya fita daga wurin, sai Dawuda ya kira shi. "Tun da na iya yanke gefen rigarka, kuma ban kashe ka ba, ka sani ka kuma gani cewa babu mugunta ko tawaye a hannuna…"

5

Shawulu ya ce a yafe shi domin yana kokari ya kashe Dawuda. Amma ba a dadde ba, tsohon halin fushinsa ya dawo sai ya shirya sojoji dubu uku domin su kashe Dawuda. Wata rana da daddare, sa'ad da sojojin suke barci, Dawuda da Abishayi, daya daga cikin sojojinsa, sun sake shigowa a gefen sansanin da Shawulu yake kwanciya yana barci.



6

"Allah ya ba da abokin gabanka a hannunka yau," Abishayi ya gaya wa Dawuda. "Ina roko bari in soke shi da mashi sau daya, har kasa: ba zan kuma soke shi sau biyu ba."



7

Dawuda ya ki. Sai ya dauki baka da goran ruwa na Shawulu, ya bar sansanin. A kan tuddu a can gefen hanya, Dawuda ya yi ihu har sai da Shawulu ya ji shi. Sau biyu kenan, Shawulu ya ga cewa da Dawuda ya so ya kashe shi da ya yi, amma bai yi ba. Sau daya kuma, Shawulu ya sake ce a yafe shi domin neman da yake ya ji wa Dawuda rauni. Amma Dawuda ya sani cewa ba zai amince da kalmomin Shawulu ba.



8

A wannan lokaci Sama’ila ya riga ya mutu.  Shi ne annabi wanda Allah ya gaya masa ya shafe Shawulu a farko, sa’an nan ya shafe Dawuda sarkin Isra’ila.  Lokacin da Filistiyawa suka kai wa Isra’ila hari, Shawulu ya yi wani abu mummuna, abin da Allah ya hana a yi.



9

Ya umarta wata mace ta kira Sama’ila daga wurin zaman matattu.  A daren nan, Shawulu ya sami sako.



10

“… UBANGIJI ya riga ya bar ka kuma yana gaba da kai... UBANGIJI ya raba ka da mulkinka daga hannunka ka, ya ba makwabcin ka, mai suna Dawuda. Gobe, da kai da ‘ya’yanka za ku kasance tare da ni.  UBANGIJI zai kuma mika sojojin Isra’ila a hannun Filisitiyawa.” Sa’ad da Shawulu ya ji wannan, sai ya summe cikin tsoro.



11

Filisitiyawa suka yi yaki da Isra’ila, sai mazan Isra’ila suka gudu.  Filistiyawa suka kashe ‘ya’yan Shawulu, hade da Jonatan, babban aminin Dawuda.



12

Shawulu ya ji rauni mai tsanani daga masu jefan baka.  Sai ya ce wa mai rika masa kayan yaki, “Ka zare takobin ka ka soke ni da shi, domin kada mugayen mutanen nan su zo su soke ni su yi mini gori.”  Amma mai kayan yakinsa ba zai iya ba, domin tsoro ya kama shi sosai.  Saboda haka, Shawulu ya dauki takobi sai ya fada a kai.



13



Sa’ad da suka samu jikunan Shawulu da ‘ya’yansa, Filistiyawa suka daura jikunan a bangon wani birnin Isra’ila wanda suka kwace.  Wadansu Isra’ilawa masu karfin hali suka kubutar da jikunan, suka dauke su zuwa gida suka kuma kone su kafin suka binne su a Isra’ila.

14



Sa’ad da Dawuda ya ji mummunan labarin, ya yi makoki da kuka da azumi har yamma don Shawulu, da Jonatan dansa, da mutanen UBANGIJI, saboda sun mutu ta takobi.

15



Ko da yake Shawulu ya yi kokari ya kashe Dawuda, Dawuda ya daukaka Shawulu a matsayin shafaffe na Allah har zuwa karshe. Yanzu, Allah ya daukaka Dawuda, ya mai da shi sarki a matsayin Shawulu.

16

**Dawuda Sarkin (Sashi 1)**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**1 Sama’ila 24-31,**
**2 Sama’ila 1-2**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

17

# KARSHE

20 60

18

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**

19